**6** Rashin fito da abubuwa kowa ya gani, musamman a wurare manya-manya da ma ƙananan wuraren ayyuka. Shin kana sane da cewa, abinda ka aikata kowa ya gani, wannnan ba zai hana ka aiwatar da lamarin rashawa ba?

**7** Dokoki da rashin kyakkyawar gudanarwa, ƙaruwar dokoki da hanyoyin kare su ba su bane mafita ba. Suna tattare ne da ƙirƙire ƙirƙiren da ƙaƙale-ƙaƙalen kalmomin masu mulki. To mene ne zai hana mu sami dokoki tsayayyu da cikakken kariyarsu a wuraren da ake gani mara kyau na rashawa. Shin wannan zai zama da wahala?

**8** Tafiyar Hawainiya da ake wa bangaren shari'a. A wasu ƙasashe, za mu ƙara da cewa, *"rashin dogaro"* ga waccan magana. Idan aka bi hanyar shari'a ɗoɗar zai zama abin koyi fiye da waɗancn da idan lokacin yanke hukunci ya zo, sai ka ga cewa ma har ana manta da laifin da aka aiwatar. Sharia'a na neman bin kadi da garanti, amma ba wai ana nufin a yi tafiyar hawainiya ga gabatar da shari'ar gaskiya. Shin muna buƙatar ƙarin masu shari'a, kuma tare da bin ƙa'idoji na kwarai?

**9** Karin girma ba bisa ƙa'ida ba. Rashawa na yaɗuwa matuƙa muddin babu tsarkin zuciya da ɗaukar nauyin da yake a wuyanmu na ƙarin girma. Ana yin biris da irin wannan hanya ce, idan an ƙarawa wani muƙami kawai saboda biyayyarsa ga ko wane ne shugaba ko waɗanda suke jagorancin jam'iyya. Ko kuma idan wannan ce hanyar su ko tsarin ma'aikatun da suke duba. Ko shakka babu wani na iya yin kuskure a yayin da yake daga muƙamin wani, amma babu matsala na rarrabewa tsakanin kuskure ƙarami da jahilci bisa ganganci ko rashin duba imani/ ra'ayi. shin wannan al'amari ne na ƙarancin hangen imani/ra'ayi?

**10** Riƙon sakainar kashi ga hukunta masu cin hanci da rashawa. Rashin baiwa hukumomi damar zartar da hukuncin da ya dace ga masu aikata rashawa, da kawo wasu hukunce-hukuncen rashawa don su zama misalai na kawo yanayi mai sauƙi na rashawa ta ci gaba da aukuwa na tsawon lokaci

A takaitace akwai dalilai da dama na shafar kai (Lamba 1 zuwa 4), na al'ada (lamba 5 zuwa 6) na ma'aikatu (lamba 7 zuwa 8) na kungiyoyi (lamba 9 zuwa 10) da aka gabato da su a mataki babba ko ƙarami ga yanayi daban-daban na al'adu da na jeranta. Kuma za mu gani a fili cewa, tantance asalin musabbabai zai inganta tare da ƙarfafa yaƙi ko faƙa da rashawa.

*Rubutawa:* **DOMÈNEC MELÉ**

# DAKARUN Cin Hanci da Rashawa




Cin hanci da rashawa wani nau'i ne na **RASHIN GASKIYA** ko **AIWATAR DA LAIFI** da mutum ko Kungiyar da aka ba shi amana suke bayarwa don samun fa'ida ta daban.







**NETWORK FOR JUSTICE**
*A Human and Consumer Rights Association*
**Tel:** 0806 553 4828 - 0803 694 2437
**Email:** networkforjustice18@gmail.com
**Website:** networkforjustice.org.ng

# NETWORK FOR JUSTICE

*A Human and Consumer Rights Association*
(Kaduna)

**JUSTICE FOR ALL**

**Tel:** 0806 553 4828 - 0803 694 2437
**Email:** networkforjustice18@gmail.com
**Website:** networkforjustice.org.ng

# Wayar Da kan AL'UMMA

## *Da Yaki A Kan*

# CIN HANCI DA RASHAWA

**da TAIMAKAWA JUNA don samar da**

**SHUGANCI NA GARI A NAJERIYA**

fNetworkForJustice
network_justice

## Game da mu

Cibiyar Nazari don Adalci (***Network for Justice***) an tsara ta a zaman tattaunawa ga duk masu son inganta ayyukan adalci da tseratar da kasar nan daga bala'in da ke jiran faruwa. ***Network for Justice*** tana fatan samar da haɗin kan jama'a waɗanda zasu taimaka wurin dakushe yaduwar rashin adalci a cikin al'umma. ***Network for Justice*** ta yi amanna cewar babu abin da zai gagari jama'a wurin fada da rashin adalci, cin hanci da rashawa a wannan lokaci da ma tarihin wannan kasar tamu.

## Manufofin mu

- Wayar da kan al'umma game da rashin adalci, dakile cin hanci da rashawa a kasarmu Najeriya, tare da bin doka da oda.
- Taimakawa masu rauni da gajiyayu da wadanda aka dannewa hakkinsu domin su samu adalci ba kawai a cikin kotuna ba, har a wurin ayyukansu na yau da kullum.
- Domin samar da jama'a masu wadatar zuci a cikin kasar nan ta wurin aminci da kowane bangare na rayuwa.
- A daukaka wayewar kasa a kan mahimmancin bunkasa halaye, dabi'u da akidu, a matakan abin da ya shafi mutum shi kanshi da na al'umma (al'umma), wadanda suke da buqatar tabbatar da adalci a cikin al'umma.
- Samar da kungiyoyin jama'a ko daidaikun mutane a cikin wannan kasa wadanda zasu bada lokacinsu don tabbatar da adalci da kare hakkin dan adam.

## Ayyukan mu

Kare Haƙƙin Ɗan-Adam, hana cin Hanci da Rashawa, Kare Haƙƙin Mallaka da wayar da kan jama'a game da 'Yancin Siyasa

A kokarin cimma burin mu, mun kirkiro da tsarin abubuwa guda hudu don farawa. Waɗannan sune kamar haka:

### KARE HAKKIN DAN ADAM

Manufar mu a wannan bangaren shine fito-na-fito da rashin adalci da akeyi ta hanyar amfani da karfin shari'a da ma'aikatan shari'a wadanda suka shafi 'yan sanda, kotuna, gidajen yari da dukkanin madafun iko da akedasu.

### YAKI DA CIN HANCI DA RASHAWA

Wannan manufar shine fallasawa da kuma yaki da cin hanci da rashawa musamman ta jami'an gwamnati wadanda (ta hanyar bugun alkalami) suke karkatar da dimbin kudaden da aka basu amana, Wannan sata da akeyi (wanda ke matukar tayar da hankali a Najeriya) ba kawai yana hana mu ingantaccen ilimi, asibitoci masu kyau, hanyoyi masu nagarta da aminci da aiyukan kyautata rayuwar jama'a ba, amma abin yafi haka muni don yakan lalata kyawawan dabi'unmu da kuma lalata dukkan al'umma .

### KARE HAKKIN ABINCI/SHA

Manufar wannan bangare shima don fallasa abubuwan haɗari waɗanda ke cikin kayayyakin abinci. Manufar shine a sanar da jama'a game da wanzuwar ƙananan ƙwayoyi cuta da magunguna marasa kyau waɗanda suka mamaye kasuwannin Najeriya. Har ila yau, ajandar ta kudurci ƙirƙiro da hanyoyin bunƙasawa da kuma wayer da kan jama'a game da hatsarin masana'antu da gurbatar muhalli ga lafiyar mutane.

### WAYAR DA KAN JAMA'A KAN DA SIYASA

Manufar wannan ajanda ita ce ilmantar da al'umma akan wajibci da kuma ingancin shiga harkokin siyasa, tare da haƙuri da rungumar juna a harkokin siyasa. Har ila yau, da zama don tattaunawa akan harkar tattalin arziki da siyasa. Dalili shine don a samu kyakkyawar alaƙa akan tsarin Najeriya na addinai da ƙabilu daban-daban.

# RASHAWA: MUSABBABAI GUDA 10




Ƙungiyar dake rajin tabbatar da adalci da gaskiya ta duniya ***(Transparency International)***, tana fitar da bayanai da ke ƙunshe da sunayen ƙasashe da suke fama da matsalar rashawa. waɗansu ƙasashen ba wai hasashe ake yi ba kawai har da tabbatar da yadda taɓarɓarewar su da samuwar cin hanci da rashawa take kara yawaita a cikin su.

Gano waɗannan dalilai ita ce hanya mafi sauki da za a bi domin ganin an daƙile yawaitar rashawa da fadadarta a cikin al'umma baki daya.

A wannan rahoton da wannan ƙungiya ta fitar a shekarar 2019 ya tabbatar mun da cewar a kwai dalilai da dama da suke taimakawa wurin yaduwa, da kuma hanyoyi da za a bi domin ganin an magance su da kuma hana aukuwar su a nan gaba.

**1** Masifaffen son tara dukiya da samun mulki ta kowane irin hali ba tare da yin la'akari da bin su yadda ya kamata a same su ba, shine hanya da ke kawo rashawa a cikin al'umma. Waɗannan ɗabi'u da al'adu suna daga cikin dalilai da suke kawo yawaitar cin rashawa ga mutane, wanda hakan kan sa mutun ya ga sai ya mallaki abubuwa ta kowace hali, yin hakan zai shafi darajar sa a wurin gaskiyarsa da riƙon amanarsa da kuma ɗabi'unsa masu kyau.

Shin mutum ya rike mutuncinsa bai fi mishi daraja akna komai ba? Shin akwai buƙatar mutum ya kasance mai addini ko samun wani ƙarfafa gwiwa waɗanda suke da karfi fiye da kare mutumci?

**2** Ragewa mutum sha'awa wacce ta wuce ɗabi'a, wannan kuwa yana faruwa ne ko dai saboda rashin ilimi ko kuma samun gurɓatacciyar fahimta a cikin abubuwan ilimin da bai inganta ba a shekarun da suka gabata. Shin ya kamata a sanya ilimin koyar da ɗa'a ga mutane? Shin ba ku ganin lokaci yayi da mutum zai gyara ɗabi'unsa na kasancewarsa mai gaskiya da sake gyaruwa ba, domin sake samun ingantanccen ilimin a gare shi?

**3** Babu wani tunanin ƙwarai a yayin da mutum ke aiki a gwamnatance ko a inda bama na gwamnati ba. Misali ana ganin hakan ga mutanen da suke amfani da siyasa domin biyan buƙatun kansu, maimakon yin amfani da siyasar don aikata alheri. Shin lokaci bai yi ba da zamu taimakawa 'yan siyasa da shuwagabanni wurin fahimtar da su yadda zasu inganta ayyukansu da gaskiya da riƙon amana?

**4** Karancin wayar da kai jama'a ko rashin ƙarfafa musu gwiwa don yin tir da Allah wadai da yin cin hanci da rashawa na daga cikin dalilai da ke taimakawa wurin kasa daƙile rashawa a cikin al'umma. Misali kamar mutum da ya san me cin rashawa ne kuma ya kama bakinsa yayi shiru. Kamar mutumin da ya san mai cin rasha ya ki nuna shi saboda yana jin tsoron rayuwarsa, ko ma ya iya cewa ai wannan matsalar bata shafe ni ba. To, shin wannan zai taimaka daƙile aukuwar rashawa nan gaba ba?

**5** Ɗabi'un al'ummar yankin da ke taimakawa cin hanci da rashawa. Irin yankin da ke taimakawa mutanen banza ko yin sha'awar aikinsu (*"sai ka zama mai wayon tsiya ko ba dole ka biya haraji ba"*) ko kuma amincewa da musun da baya da alheri kamar (*"ai kowa yana aikatuwa" "yi amfani da damar da ka samu rayuwar nan bata da tabbas"*). Wanene yakamata ya inganta wannan al'adar? Shugabannin zamantakewa? Kowa? Shugabannin al'umma? Kowa da kowa?